**Rahoton tsirren da aka bunkasa kwayar halittarsu da aka kasuwntar watau GM crops na shekara ta 2013**

**Wallafawar Clive James, wanda ya kirkiri kungiya kuma shugban ISAAA**

*Wannan saudaukarwa ce ga marigayi Norman Barloug daya lashe Kyautar zaman lafiya ta Laureate kuma uba ga kungiyar ISAAA domin cika shekaru 100 da haihuwarsa a ranar 25 ga watan Maris na shekara ta 2014*

---

**BAYANAI 10 DA YAKAMATA KU SANI GAME DA tsirren da aka bunkasa kwayar halittarsu a shekara ta 2013**

**Bayani na 1. Shekara ta 2013 itace shekara ta goma sha takwas (18) da aka samu nasarar kasuwantar da tsirren da aka bunkasa kwayar halittarsu.** An fara amfani da tsirren da aka bunkasa kwayar halittarsu ne a matsayin hanyar kasuwanci a shekara ta 1996. kuma a duk shekara an samu bunkasar wannan harka tun daga shekara ta 1996 har zuwa shekara ta 2013 kuma a cikin shekaru sha biyu (12) an samu bunkasa na sama da kashi goma cikin dari,(10%) haka ya bayyana karara akan irin yarda da kwarin gwiwa da manoma suke dashi akan wannan tsirrai a kasashen masu arzikin masana'antu da kuma masu tasowa dake fadin duniya. hakika an samu gagarumin cigaba tun daga ranar farko da ka shuka irin wannan tsiro a shekara ta 1996 sai da ta kai an girbi amfanin daya kai na Hekta miliyan dubu daya (1) da digo biyar (5) a filin noma daya linka fadin kasar Amurka ko kasar Sin sau 50 idan aka kwatanta da kasashen biyu

**Bayani na 2. a tsirren da aka bunkasa kwayar halittarsu sun bukasa da ninki hari dari (100) daga hekta miliyan daya da digo bakwai (1.7 miliyan) a shekara ta 1996 zuwa hekta sama da miliya 175 a shekara ta 2013.** Hakan yasa fasahar bunkasa halittar tsirrai ta kasance fasahar da mutane suka fi amfani da ita a kwana kwanan nan-saboda dalilin moriyar da ake samu daga gareta. A shekara ta 2013 an samu karuwar hektoci miliyan biyar (5) na tsirren da aka bunkasa kwayar halittarsu a shekara ta 2013 watau a duk shekara ana samun bunkasa kashi uku (3) cikin dari musamman yadda wannan tsari ya samu karbuwa sosai da kashi casa'in zuwa kashi dari (90-100%)

**Bayani na 3.kasashe da yawa na noma tsirren da aka bunkasa kwayar halittarsu d kuma tara tsirran da yawa.** A ciki kasashe 27 da suka noma tsirren da aka bunkasa kwayar halittarsu a shekara ta 2013 19 daga cikinsu kasashe ne masu tasowa a yayinda 8 kawai masu arziki Masana'antu. wadannan kasashe sun noma Hekta miliyan 47 da dubu daya ko kuma kashi 27 cikin dari na abinda aka noma a shekarar data gabata

**Bayani na 4. A karo na biyu a shekara ta 2013 kasashe masu tasowa sun zarce kasashe masu arzikin masana'antu wajen noma tsirren da aka bunkasa kwayar halittarsu.** Kasashe masu tasowa a bara sun noma abinda ya kai kashi (54%) Hamsin da hudu cikin dari (hekta miliyan casa'in da hudu 94) na tsirren da aka bunkasa kwayar halittarsu a fadin duniya a inda kasashe masu cigaban masana'antu suka noma kashi arba'in da shidda (46%) cikin dari (watau hekta miliyan tamanin da daya 81). a bara kasashe da dama sun samu nasarar hadin gwiwa tsakanin gwamnati da kuma kanfanoni masu zaman kansu kan wannan shiri, wadandan kasashe kuwa sune Brazil Bangladash da Indonesia

**Bayani na 5. An samu karuwar manoma dake Noma tsirren da aka bunkasa kwayar halittarsu.** A shekara ta 2013 akalla manoma miliyan sha takwas (18) suka noma tsirreen da aka bunkasa kwayar halittarsu wtau karin kashi digo bakwai cikin dari (.7%) kan manoma da suka yi hakan a shekara ta 2012 - kuma abin alfahari sama da kashi casa'in (90%) cikin dari na manoman watau manoma miliyan sha shidda (16) da digo 5 kananan manoma ne kuma matalauta a kasashe masu tasowa. wadannan manoma sunyi amfani da dubaru daban-daban wajen kare matsaloli kala-kala domin samun nasara da hakan ya kare matsalar sare dazuzzuka. a shekara ta 2013 kimanin kananan manoma miliyan bakwai (7) da dubu dar biyai (5) a kasar Sin da kuma manoma miliyan bakwai (7) da dubu dari uku (3) a kasar Indiya suka zabi su noma irin auduga wadda aka bunkasa kwayar halittarta a hekta miliyan sha biyar (15) a dalilin moriyar da suka samu daga wannan tsarin. Haka kuma a shekara ta 2013 kimanin manoma dubu dari hudu (400) a kasar nan Philippines suka samu moriyar ingattacen irin masara.

**Bayani na 6. Manyan kasashen dake amfani da fasahar bunkasa halittar tsirrai sunyi amfani da fasahar wajen shuka irin masaarar dake jurewa rashin ruwa na fari da kuma wani irin waken suya sanfarin HT/IR.** Kasar Amurka har yanzu tana a matsayi kasa ta daya kuma kasa ta farko a fadin duniya, data Noma abinda ya kai Hekta miliyan saba'in (70) da dubu dari daya (1) da samun karbuwa data kai kashi casa'in (90%0 cikin dari na dukkan kayan abinci. Babban abu mai mahimmanci shine sama da manoma Amurka dubu biyu (2) ne suka noma irin masarar nan dake jurewa karancin ruwa na fari a filin noman daya kai Hekta dubu hamsin (50). Kasar Brazil har yanzu tana a matsayin kasa ta biyu dake bin bayan kasar Amurka a cikin shekaru biyar a matsayin kasar dake amfani da fasahar bunkasa halitattar tsirrai sannan kasar ta kasance kan gaba a matsayin kasar da akullum ke bunkasa amfani da wannan fasaha a tsakankani kasashe a fadin duniya domin ko a bana abin sha'awa sai da ta kara yawan Hekta miliyan (uku) 3 da dubu dari bakwai (7) kan shekarar ta 2012 watau an samu karin kashi goma (10%) cikin dari kan abinda aka noma a bara da hakan yasa yanzu kasa na amfani da filin noman daya kai Hekta miliyan arba'in (40) da dubu dari uku (3) kenan. sannan a bana kasar ta Brazil a karon farko ta shuka irin waken suya nan safarin HT/IR da yakai na hekta miliyan biyu (2) da dubu dari biyu (2) bayaga wani irin wake na cikn gida da kasar ta inganta da zai iya bijirewa kwayar cutar nan ta bairos da yanzu haka ake gaf da a kasuwantar dashi. Kasar Argentina itace a matsayin kasa ta uku (3) dake Noma abinda yakai hekta miliyan ashirin da hudu (24) da dubu dari hudu (4). Sai kuma kasar Indiya da a bana tasha gaban kasar Kanada a matsayin kasa ta hudu (4) dake noma abinda yakai Hekta miliyan sha daya (11) na Audugar da aka bunkasa kwayar halittarta data samu karbuwar na kashi casa'in da biyar (95%) cikin dari. Sai kasar Kanada da a yanzu ta koma a matsayin kasa ta biyar (5) dake noma Hekta miliyan goma (10) da dubu dari takwas (80 da a bana aka samu raguwar noma irin nan na canola amma da karbuwar data kai ta kashi casa'in da shidda (96%) cikin dari. A shekara ta 2013 kowace kasa daga cikin wadannan kasashe biyar (5) da suke kan gaba wajen amfani da wannan fasaha ta bunkasa kwayar halittar tsirrai ta noma abinda ya zarce Hekta miliyan goma (10) kowanensu hakan nema ya dasa kyakyawan harsashin amfani da wannnan fasaha domin samun cigaba a shekaru masu zuwa.

**Bayani na 7. Africa Matsayin fasahar tsirren da aka bunkasa kwayar halittarsu a Nahiyar Afrika.** Nahiyar Afrika na cigaba da samun bunkasa kan wannan fasaha da kasar Afrika ta kudu ta samu moriya na tsirren da aka bunkasa kwayar halittarsu a sama da shekaru goma (10), kasashen Burkin Faso da Sudan dukkaninsu sun bunkasa yawan Hektocin da suke noma irin Auduga da aka bunkasa kwayar halittarta daga kashi hamsin (50%) cikin dari zuwa Kashi dari uku (300) a shekara ta 2013 sannan wasu kasashe Bakwai (7) kuma (watau kasashen Kamaru da Misra da Ghana da Kenya da Malawi da Najeriya da kuma Uganda) sun gudanar noma na kwaji da hakan zai bayar da dama don kasuwantar da amfani da wannan fasaha ga manoma, abun mafi muhimmaci shine cewa shirin nan na WEMA a karon farko zai samar irin Masarar nan dake jurewa rashin ruwa na fari a shekara ta 2017. rashin kayan aiki da cikakken tsari na kimiyya a wannan Nahiya ta Afrika na cigaba

da kasancewa babban matsalar da hana samu karbuwar wannan fasaha a Afrika. Ana bukatar ingatattun dokoki wadanda suke ba tsaurara ba musamman ga kanana kuma matalautan Manoma domin kawo cigaba a kasashe masu tasowa.

**Bayani na 8. Matsayin tsirren da aka bunkasa kwayar halittasu a Tarayyar Turai.** Kasahe biyar (5) na Tarayyar Turai ( watau Spain da Portugal Da czech Republic da Slovakia da kuma Romania) ne suka shuka abinda yakai Hekta dubu dari da arba'in da takwas da goma sha uku (148013) na irin Masarar da ka bunkasa kwayar halitarta da aka samu karin kashi sha biyar (15%) cikin dari kan abinda aka noma a shekara ta 2012. kasar Spain itace kan gaba a Tarayyara Turai data noma Hekta dubu dari da talatin da shidda da dari tara da sittin da biyu (136962) na irin masarar da aka bunkasa kwayar halittarta watau karin kashi sha takwas (18) cikin dari na abinda kasar ta Noma a bara da kuma ya samu karbuwa da kashi talatin da daya (31%) cikin dari a karon farko a shekara ta 2013

**Bayani na 9. Moriyar da aka samu daga tsirren da aka bunkasa kwayar halittarsu.** Daga shekara ta 1996 zuwa shekara ta 2012 wannan fasaha ta bunkasa kwayar halittar tsirrai ta tallafa wajen samar da isashen abinci, sannan  ta tallafa wajen kiyaye muhalli da hana zafafar yana ta wajen- ta wajen samar da kayan abincin da darajarsu ta kai ta Dala miliyan dubu dari da goma sha shidda (116)  da miliyan dari (9), sannan ta kyautata muhalli ta rage amfani da maganin kwarin daya kai Kilo miliyan dari hudu da casa'in da bakwai (497) a shekara ta 2012 kawai wannan fasaha ta rage amfani da gurbatacciyar Iskar gas data Kilo miliyan dubu ashirin da shidda (26) da digo bakwai (7) watau kwatankwacin dakatar da mota miliyan sha daya (11) daga kan tituna na tsawon shekara a dalilim hayakin da suke fitarwa, haka wannan fasaha ta tallafawa rage sare dazuka domin fadada filin noma da hekta miliyan dari da ashirin da uku (123) daga shekara ta 1996 zuwa 2012, da kuma tallafawa yaki da fatara ga kananan Manoma miliyan sha shidda (16) da digo biyar (5) da iyalansu da suka kai miliyan sittin da biyar (65) wadanda wani bangare na mutanen da suka fi fama da fatara a fadin duniya. Hakika Tsirren da ka bunkasa kwayar halittarsu na da kyau kwarai harkar noma sai dai wannan fasaha bata dace ba da ingatancen dubarun noma ba, kamar jujjuya abinda ake nomawa a duk shekara, da dubarar kare kangarewa daga tsirrai wadanda wannan aka saba dasu na yau da kullum.

**Bayani na 10. Hasashen Cigaba.** Akwai hasashen samun cigaba kwarai akan fasahar bunkasa tsirrai musamman na karbuwar daya samu data kai kashi casa'in (90%) cikin dari ko kuma sama da haka a kasuwannin kasashe masu tasowa kai harma da wadamda keda arzikin masana'antu. Kasashen Bangladash, da Indonesia da kuma Panama dukkaninsu sun amince da tsirrai da aka bunkasa kwayar halittarsu a shekara ta 2013 da kuma shirin kasuwantar dasu a shekara ta 2014.

ISAAA kungiya mai zaman kanta da ka kafa ba don samun riba ba, da hadin gwiwar hukumomin gwamnati da masu zaman kansu ke daukar nauyi. dukkan kiyasin Hektocin tsirren da aka bunkasa kwayar halittarsu da aka lisafta a sama a kiga sune sau daya kawai, ba tare da la'akara da ababen da dunkule da kayan gonar ba.Za'a iya samun  cikakken bayanai a ISAAA Brief 46 na rahoton tsirren da aka bunkasa kwayar halittarsu na kasuwa a fadin duniya  GM crops na shekara ta 2013 da Clive James ya wallafa domin karin bayani sai a ziyarci adireshinmu dake yanar gizo na www.isaaa.org ko cibiyarmu ta ISAAA SEA +63 49 536 7216, ko cibiyarmu ta ISAAA Afri +254 20 422 3618 ko adreshin email na africenter@isaaa.org.